

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Maganin Kiyayya

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Na gaskata cewa sakamakon farko na ƙiyyaya shi ne gaza karɓar ƙauna ko nunawa. Babu wani ɗaya daga cikin mu da zai iya nuna ƙauna sai dai idan ya fara karɓar ƙauna. Yahaya ne ya yi wannan magana a cikin Sabon Alƙawari, lokacin da ya rubuta:

> "Muna ƙauna domin shi [wato,Allah] ne ya fara ƙaunarmu" (1 Yahaya 4:19)

Ban yarda cewa wani zai iya nuna ƙauna idan ba a ƙaunace shi da farko ba. Ta haka, mutumin da ba a taba ƙaunarsa ba, ba zai iya nuna ƙauna ba.

Sakamakon ƙiyayya na biyu su ne manyan hanyoyi guda uku da mutane ke mayar da martani ga ƙiyayya: na farko, akwai mutumin da ya sadakar; na biyu, akwai mutumin da ke haƙuri; na uku kuma, akwai mutumin da ke ramawa.

Waɗannan hanyoyi uku na mayar da martani ga ƙiyayya suna da wani abu iri ɗaya. Kowannensu mai kariya ne, da yake ɓoye ɓacin rai. Babu ɗaya da ke da mafita mai kyau. Amma, Allah yana da kyakkyawar mafita.

A cikin Ishaya 61:1, mun sami alƙawarin da aka cika ta wurin zuwan Yesu Almasihu:

> "Ruhun Ubangiji yana bisa na, saboda Ubangiji ya zabe ni, ya aike ni domin in kawo albishir mai daɗi ga talakawa; in warkar da waɗanda suka karai a zuci, in yi shelar kwance ɗaurarru, da kuma 'yanci ga waɗanda suke cikin kurkuku"

Wajen cika wannan alƙawari, Allah ya tanada maganin ƙiyayya. Ya zo gare mu ta wurin Yesu da gicciye. Shirin Allah na har abada, har ma kafin halitta, shi ne domin mu zama 'ya'yansa—'ya'yansa maza da mata. Lokacin da Yesu ya ɗauki zunubanmu ya kuma sha wahala don ƙiyayyar mu, Ya buɗe hanya don karɓarmu ta wurin Wanda amincewarsa take da muhimmanci.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa na fita daga sakamakon ƙiyayya, maimakon haka ina karɓar maganin da Allah ya tanadar mani ta wurin Yesu

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Kristi Almasihu. Ina furta cewa Yesu ya ɗauki ƙiyayya ta domin in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-142-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.